JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA 1 Sha'aban, 1443
MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI 4 Maris, 2022

(1)

# TASIRIN ZAKKA DA SADAKA WAJEN HAVAKA RAYUWAR ZAMANTAKEWA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Ku tsayar da Sallah, ku kuma bayar da Zakka, ku kuma yi ruku'i tare da masu ruku'i)** [al-Baƙra: 43], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai shari'ar Musulunci ta sanya wa mutane wani daidaitaccen tsari na zamantakewa, wanda ya ginu akan harsashen tausayi da haɗin kai da taimakon kumar, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Misalin muminai a wajen soyayyar juna da tausayin juna da ƙaunar juna kaman jiki ne da idan wata gaɓa ta sami matsala dukan jikin yake kamuwa da rashin barci da zazzaɓi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai idan abincin ƙabilar Ash'arawa ya tashi ƙarewa a lokaci yaƙi, ko abincin iyalansu ya yi ƙaranci a garin Madina; sai su tattara dukan abin da suke da shi a tufafi ɗaya, sannan sai su raba mudu mudu daidai wa daida a tsakaninsu, su nawa ne, ni ka nasu ne).**

Ta haka ne Musulunci ya shar'anta Zakka, ya kuma sanya ya zama ɗaya daga cikin rukunnansa, ya kuma kwaɗaitar da a yi sadaka, ya kuma sanya ta cikin manyan ƙofofin alhairi, saboda

rawar da take takawa wajen biyan buƙatun mabuƙata, da yaye masu damuwa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ka amshi sadaka daga cikin dukiyoyinsu da za ka tsarkake su da ita)** [al-Tauba: 103], haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Duk wani abu da kuka ciyar Allah zai kwafe maku makwafin sa, lallai shi ne fiyayyen masu azurtawa)** [Saba'i: 39], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(An gina Musulunci akan abubuwa guda biyar: Shaida babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah, kuma Annabi Muhammadu Manzon Allah ne, da tsayar da Sallah, da bayar da Zakka, da Hajji, da Azumin watan Ramadhan).**

Duk wanda yake yi wa Alƙur'ani mai girma kallo na lura zai ga inda Allah Mabuwayin Sarki yake gwama Zakka a wurare masu yawa da manyan farillai, masu matsayi na musamman, an gwama ta da Sallah saboda kwaɗaitar wa game da ita, Allah Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Ku tsayar da Sallah ku kuma bayar da Zakka, duk wani aikin alhairi da kuka gabatar wa kawunanku za ku taras da shi a wurin Allah, lallai Allah yana da cikakkiyar masaniya akan abubuwan da kuke aikatawa)** [al-Baƙra: 110], haka ma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Su ne waɗanda suke tsayar da Sallah, suke kuma bayar da Zakka, suna kuma da cikakken yaƙini da zuwan ranar lahira)** [al-Baƙra: 4].

Haka ma Shari'ar Musulunci da zo da gargaɗi ga waɗanda ba sa bayar da Zakka, Allah Mai Tsarki yana cewa: **(Kada waɗanda suke rowa da abin da Allah ya ba su na dukiya saboda falalar sa, ba kuma sa ciyar da ita wajen aikata wajibi da hanyoyin alhairi, kada su zaci cewa hakan alhairi ne a gare su, a'a, hakan sharri ne da yake da mummunar makoma a gare su, za a saka masu da mummunan sakamako a ranar alƙiyama, za su kasance**

**cikin azaba a duk inda suke, komai da yake cikin duniya zai koma mallaka ne na Allah Maɗaukakin Sarki, lallai shi Allah Maɗaukakin Sarki ya san abin da kuke aikatawa, da sannu zai saka maku da shi)** [Ali Imran: 180], Haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai waɗanda suke tattara dukiyoyi na zinare da azurfa, suke taskace su, ba tare da sun fitar masu da zakka ba, to ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), ka yi masu gargaɗi da azaba mai tsananin raɗaɗi. A ranar alƙiyama za a kunna wa wannan dukiyoyi wuta a cikin jahannama, sannan da wannan ƙonannun dukiyar za a yi wa masu shi lalas a fuskokinsu, da sassan jikkunansu da bayansu, sai a rinƙa cewa masu: wannan fa shi ne abin da kuka adana wa kawunanku, ba ku fitar da haƙƙin Allah daga ciki ba, saboda haka a yau ku ɗanɗani azaba mai tsanani)** [al- Tauba: 34 - 35], Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) yana cewa: Abubuwa guda uku, gwame suke da abubuwa uku, ba a amsar ɗaya sai da 'yar uwarta, **(Ku bi Allah, ku kuma bi Annabi)**, duk wanda ya bi Allah bai bi Annabi ba ba za a amshi biyayyarsa ba, **(Ku tsayar da Sallah ku kuma bayar da Zakka)**, duk wanda ya yi Sallah bai yi Zakka ba, ba za a amshi sallarsa ba, **(Ka gode mini, ka kuma gode wa iyayen ka)**, duk wanda ya gode wa Allah bai gode wa iyayensa ba, shi ma ba za a amshi gidiyarsa ba.

Babu shakka kan cewa lallai sadaka tana ƙarfafar rawar da Zakka take takawa wajen cigaban al'umma, saboda haka ne Shari'a ta zo ta yi kira da kwaɗaitarwa game da ita, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai akwai wani haƙƙi a cikin dukiya wanda ba Zakka ba ne)**, sannan ya karanta inda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **(Kai, lallai**

**mutane sun yawaita magana akan al'amarin alƙibla, kai kã ce ita ce alhairi ita ɗaya kacal, wannan kuma ba shi ne gaskiya ba, ba fuskantar wani sashe a gabãshi ko yammaci shi ne kashin-bayan addini ko matattara alhairi ba, matattara alhairi yana cikin abubuwa ne masu dama, wasu suna cikin rukunnan ingantacciyyar aƙida ne, wasu kuma suna cikin tushen ayyuka na gari da ibadu. Na farko shi ne: imani da Allah, da ranar tashin alƙiyama, da hisabi, da abubuwan da za su biyo bayan haka a ranar alƙiyama, da imani da mala'iku da littattafan da aka saukar wa Annabawa, da ma su kansu Annabawan. Na biyu shi ne: bayar da dukiya cikin jin daɗin rai ga talakawa, makusanta da marayu da waɗanda buƙatu da rashi suka yi masu yawa, da matafiyan da guzuri ya yanke masu, ba su da abin da zai isar da su zuwa ga manufarsu, da masu roƙon mutane da buƙata ta tilasta masu yin haka, da kuma ciyarwa don manufar 'yanta bayi da 'yanta wuyayensu ga barin bauta. Na uku: kiyaye sallah. Na huɗu: fitar da zakkar da aka wajabta. Na biyar: cika alƙawari a rai da dukiya. Na shida: haƙuri akan cutar da za ta faɗa wa rai ko dukiya, ko lokacin haɗuwa da abokan gaba a wurin yaƙi. Waɗanda suka haɗa waɗannan aƙidu da ayyuka na alhairi su ne waɗanda suka yi gaskiya cikin imaninsu, su ne waɗanda suka ji tsoron kafirci da ƙasƙanci, suka kuma nesance su)** [al- Baƙra: 177].

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai Zakka da sadaka suna da matuƙar amfani, a cikin amfanin su akwai: samun albarka da lada Mai yawa, Allah Mai girma yana cewa: **(Allah yana ɗebe albarkar riba, yana kuma haɓaka Zakka)** [al- Baƙra: 276], Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai waɗanda suka yi imani, suka kuma aikata ayyuka na gari, suka tsayar da Sallah, suka kuma bayar da Zakka, suna da lada mai girma a wurin Ubangijinsu, ba za su ji tsoron komai ba, ba kuma za su sami damuwa ba)** [al- Baƙra: 277], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk ranar da bayi suka wayi gari akan sami wasu mala'iku guda biyu da suke saukowa suna addu'a, ɗayan cikin su ya ce: Ya Allah Ubangiji ka bai wa duk wani mai ciyar arziki akan abin da ya ciyar, ɗayan kuma yana cewa: Ya Allah Ubangiji, ka haɗa ƙanƙamo da asara)**.

Haka ma a cikin amfanin akwai kasancewarta hanyar samun lafiya, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ku yi wa marasa lafiyar cikin ku magani ta hanyar yin sadaka, ku kiyaye dukiyar ku ta hanyar yin Zakka, ku shirya wa bala'i ta hanyar addu'a),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai sadaka tana butar da fushin Ubangiji, tana kuma tunkuɗe mummunar mutuwa).**

Lallai Zakka tana da rawa mai girma da take takawa wajen samun daidaito a rayuwar zamantakewa, da samar da ayyukan raya ƙasa, tana kuma ƙara faɗaɗa a fagen sadaka, sawa'un sadaka mai gudana ne, ko kuwa sadaka da ma'anarta mai faɗi, ko kuwa ya zo a ƙarƙashin wani shiri kaman shirin samar da naman layya ga mabuƙata, ko sanya hannu wajen samar da abinci a gare su, ko samar masu da barguna a lokacin sanyi, ko samar masu da gidaje, ko daman samun aikin yi, da dai sauransu cikin hanyoyin

biyayya da suke bayar da gudummawa wajen bayar da kulawa ta musamman da iyalan da suka fi buƙatar taimako.

Lallai muna matuƙar buƙatar tabbatar da ma'anonin biyayya da sada zumunta da gabatar da taimako a aikace, matuƙar muna son soyayyar juna ta yaɗu, arziki ya yawaita, a kuma sami ayyukan raya ƙasa da more rayuwa..

**Ya Allah Ubangiji ka kiyaye mana ƙasar mu da sauran ƙasashen duniya.**